# Littafi mai Tsarki na yara

**Ke gabatar da**

# Dawuda Saurayi Makiyayi



**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Lazarus**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Ruth Klassen**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan**
**har ba zaku sayar da shi.**

**Tun tun da, a kwanakin Sarki Shawulu na Isra’ila, wani yaro mai suna Dawuda ya taimake ‘yan’uwansa bakwai lura da tumakin babansu. Ko da yake shi ne dan karamin, Dawuda yana da karfi, da karfin hali wanda yana kaunar Allah ya kuma amince da Allah.**



**Zaki ya taba kai wa tumakinsa hari domin ya cinye dan tunkiya na abincin yamma. Saurayi Dawuda ya kai wa mai kawo hari hari.  Ya janye dan tunkiyan daga zakin, ya cafke dabban ta gemunsa ya kashe shi. Dawuda ya sani cewa Allah ne ya taimake shi.**



Sama’ila, annabin Allah, yana cikin bakin ciki har yanzu cewa Shawulu ya ki ya yi wa Allah biyayya sosai. “Har yaushe za ka bar makoki don Shawulu?” Allah ya tsawata wa Sama’ila. “Ina aike ka zuwa wurin Yesse… Gama na tanada wa kaina sarki a cikin ‘ya’yansa maza.” Yesse shi ne baban Dawuda.



Ko da yake Sama'ila ya san Sarki Shawulu zai iya kashe shi don zuwa neman wani sarki, annabin kuwa ya yi biyayya ga Allah.





Sa’ad Sama’ila ya iso, Yesse ya sa ‘ya’yansa bakwai sun wuce a gaban Sama’ila. Amma Sama’ila ya ce wa Yesse, “UBANGIJI bai zabe wani daga wadannan ba.” Wannan ya bar Dawuda ne ya rage, shi ne auta. Yana a fili yana kiwon tumaki. Sai aka kawo Dawuda ciki. Sai UBANGIJI ya ce, “Tashi, ka shafe shi; gama wannan shi ne.”

A gidan sarki na Shawulu, Ruhun UBANGIJI ya riga ya bar wurin, Shawulu kuma ya zama mutum mai damuwoyi. ‘Yan hidimarsa suna tunanin kadekade da rayeraye mai kyau zai kwantar wa Shawulu zuciya. Daya daga cikinsu ya san wani saurayi wanda ya iya buga mollo da kyau. Ko za ka iya tuna ko wane ne wannan saurayin? I’i, Dawuda ne.



**Muzikan Dawuda ya kwantar wa Shawulu zuciya ya kuma taimake shi ya yi tunani daidai.  Shawulu ya gaya wa Yesse ya bar Dawuda ya zauna a gidan sarki yana hidima.  Duk lokacin da Shawulu ya sami hari daga bacin rai da tsoro, sai Dawuda ya buga masa mollon.  Ya kan yi taimaka.**



**Bayan da Dawuda ya tafi gida, Shawulu ya kasance da damuwa da Filistiyawa. ‘Yan’uwan Dawuda suna cikin sojoji masu fada wa Shawulu. Yesse ya aiki Dawuda zuwa bakin daga domin ya kai musu abinci ya kuma ji ko yaya ne suke.**



**Wani KATO dogon mutumin Filistiya, mai suna Goliyat, ya riga ya ba wa duka sojojin Isra'ila tsoro.**



**“Ku zabi mutum da kanku bari ya gangara zuwa wuri na!” Goliyat ya yi ihu. “Idan har ya iya fada da ni har ya kashe ni, to za mu zama bayinku. Amma idan na kashe shi, to, za ku zama bayinmu ku yi mana hidima.” Duka mazan Isra’ila, sa’ad da suka ga katon mutumin, suka gudu daga gareshi cike da tsananin tsoro.**



**Sai Dawuda ya ce wa Shawulu, “Kada zuciyar wani ya karaya saboda shi, dan hidimarka zai tafi ya yi fada da wannan mutumin Filistiyan.” Shawulu ya so Dawuda ya sa rigunan yaki ya kuma rike takobi. Maimakon haka, Dawuda ya dauki majajjawarsa sai ya dauki duwatsu biyar masu laushi daga bakin wani wurin ruwa.**



**Goliyat ya yi dariya sa'ad da ya ga dan saurayi Dawuda bai ma saka rigunan yaki ba. "Zan ba da naman jikinka wa tsuntsaye da dabbobin filayen daji!" yana kururuwa.**



**"Na zo gareka a cikin sunan UBANGIJI!" Dawuda ya amsa. "Wannan rana UBANGIJI zai mika ka a cikin hannuna… gama yakin na UBANGIJI ne!"**



**Sa'an nan Dawuda ya gudu zuwa wurin Goliyat. Sa'ad da yake gudu, sai ya harba dutse daya daga majajjauwarsa – har cikin goshin Goliyat. Goliyat ya fadi har kasa!**

Da sauri-sauri Dawuda ya cire katon takobin Goliyat ya yanke kan Goliyat. Sa’ad da Filisitiyawa suka gan cewa Goliyat ya mutu,  sai suka gudu domin su tsira da ransu.



Sarki Shawulu bai tuna cewa wannan Dawuda ne ya yi masa jinya da molo ba. Ya sa Dawuda ya lura da sojojinsa – sai ya fara kishi sa’ad da mutane suka fara yi wa Dawuda kirari a kan nasarorinsa a yaki. “Yanzu me ya rage wanda zai samu in ba mulkin ba?” Shawulu ya yi tunani. Saboda haka daga ranar, Shawulu ya fara sa wa Dawuda ido.





Kuma, Sarki Shawulu ya damu sosai a cikinsa.  Sai Dawuda ya buga masa muzika domin ya kwantar masa da zuciya.  Sau uku Shawulu ya jefi Dawuda da mashinsa.  Amma Dawuda ya kubuta har sau uku.



Shawulu yana tsoron Dawuda, saboda ya sani cewa UBANGIJI yana tare da shi, amma ya riga ya rabu da Shawulu.



**Amma Jonatan, yaron Shawulu, ya so Dawuda kamar dan'uwansa. "Babana Shawulu yana nema ya kashe ka," ya gargadi Dawuda. Sai Dawuda ya gudu. Matarsa ta gyara wani abu kamar mutum sai ta saka gadonsa, sai ta sa Dawuda ya bi ta taga a tsakar dare. Sa'ad da mutanen Shawulu suka zo da safe, Dawuda ya riga ya gudu.**



Dole Dawuda ya gudu da nesa daga Shawulu. Kafin ya gudu, da shi da Jonatan suka yi yarjejeniya tare. Sun yi alkawari za su yi ta taimaka wa juna a kullayomi. Abin bakin ciki, abokai biyun suka yi ban kwana da juna.

Dawuda ya tafi domin ya nemi inda zai zauna ban da tsoron cewa sojojin



# Dawuda Saurayi Makiyayi

## Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki

## a na samu a

## 1 Sama’ila 16-20

**“Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske.” Zabura 119:130**

# KARSHE

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**